Mun yi sahur tare da Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -, sannan ya tashi zuwa sallah, na ce: Nawa ne tsakanin kiran sallah da sahur? ya ce: Gwargwadan ayoyi hamsin

Daga Zaidu ɗan Sabit - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Mun yi sahur tare da Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -, sannan ya tashi zuwa sallah, na ce: Nawa ne tsakanin kiran sallah da sahur? ya ce: Gwargwadan ayoyi hamsin.

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Wasu daga sahabbai - Allah Ya yarda da su - sun yi sahur tare da Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -, sannan tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya tashi zuwa sallar Asuba. Sai Anas ya cewa Zaid ɗan Sabit - Allah Ya yarda da shi -: Nawane gwargwadan lokaci sahur tsakanin kiran sallah da iƙama? Sai Zaid ɗan Sabit - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Gwargwadan karanta ayoyi hamsin ne matsakaita, ba dogwaye ba ba kuma gajeru ba, ba karatu da gaggawa ba ba kuma a hankali ba.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/4457